# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Cin zarafi ta hanyar lalata tsakanin al'umma a Afirka
## Kashi na bakwai: Lokacin ɗaukan mataki


| | |
|---|---|
| Wanda ya rubuta: | Chrispin Mwakideu |
| Wanda ya fassara: | Yusuf Idris |
| Wadda ta tace: | Halima C. Schmaling |


**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Hadiza: | 'yar shekara 30 |
| Dauda: | ɗan shekara 40 |
| Malama Talatu: | 'yar shekara 45 |
| Adams: | ɗan shekara 10 |
| Fati: | 'yar shekara 16 |
| Tanko: | ɗan shekara 45 |
| Julie: | 'yar shekara 40 |
| Jammo: | ɗan shekara 45 |
| Ofisa: | ɗan shekara 45 |

**Mai gabatarwa:**

Masu sauraronmu, barkanmu da sake saduwa da ku a cikin wannan shirinmu na "Ji Ka Karu" wanda muke kawo muku a kan cin zarafin mata da yadda yake aukuwa a ƙasashenmu na nahiyar Afirka. A cikin shirin da ya gabata kun ji yadda malamar su Adams ta gayyaci mahaifiyar Adams ɗin, wato Precious, saboda tana tunanin cewa ana cin zarafin Adams ɗin a gida. Tattaunawar da suka yi dai ba ta ƙare da arziki ba. Precious ta ƙaryata cewa ba wani abu na muni da saurayinta Jammo yake yi wa ɗanta.

A wani wurin kuma, Julie ta kai ziyara makarantar su Fati, inda ta yi musu bayani a kan cin zarafin 'ya mace da tilasta wa 'ya'ya mata yin jima'i. A daidai lokacin da ta shiga motarta za ta tafi, sai Fati ta garzayo a guje, tana kuka, tana roƙon Julie cewa ta tsaya. Me zai faru a gaba? Abin da za ku ji ke nan a yau a cikin shirin mai taken "Lokacin ɗaukan mataki" wanda kuma shi ne na bakwai.

Za mu faro ne daga wurin Hadiza, wadda ta sha da ƙyar daga fyaɗe da 'yan ta'adda suka yi mata, kuma an sallame ta daga asibiti makwanni kaɗan da suka gabata, amma dai abubuwa ba sa tafiya daidai tsakaninta da mijinta Dauda.

**Fitowa ta 1: A gidan Dauda da Hadiza**

**Hadiza:** Dauda, don Allah! Don Allah, kar ka tafi! Kai kaɗai ka fahimce ni. 'Yan sanda sun ƙi taimakona, illa ma dai sai suka mai da ni kamar wata sakarya. Duk kawayena sun guje ni.

**Dauda:** Hadiza, sai dai fa ki yi haƙuri, amma ko barazanar da kike yi na kashe kanki bai isa ya sa in ci gaba da zama da ke ba.

**Hadiza:** Amma Dauda, ba zan iya jure wa wannan al'amarin ni kaɗai ba. Kai ka ga abin da suka yi min! Ka san yadda aka

yi nake ci gaba da rayuwata a kullu yaumin? Ko da yaushe a tsorace nake! Da na ga gungun maza sai jikina ya fara rawa. Kai kaɗai na yarda da shi. Saboda kai ka ceto ni. Ba don ka zo nemana ba da na mutu a bakin rafin nan. Dauda mijina, don Allah kar ka tafi ka ƙyale ni!

**Dauda:** Saurara ki ji, Hadiza. Ba na son in zama maras tausayi. Amma a yanzu, ba wanda yake so ya yi wata dangantaka da ke saboda abin da ya faru. Sannan kuma saboda ni ne mijinki, ni ma ba wanda yake so ya dinga wata hulɗa da ni. Ni kuma dole ne in ci gaba da rayuwata!

**Hadiza:** Me ya sa za ka yi haka?! E?! Kai kana da zaɓin ka tafi ka ƙyale ni kuma ka yi, amma ni kuma ba yadda za a yi rayuwata ta koma kamar da! … Tafi ka ci gaba da rayuwarka Dauda!

**Dauda:** Hadiza, ya kamata ki nemi taimako! Akwai wata mata da aka ba ni labarinta, sunanta Julie. Tana da wata ƙungiya a birni, kuma tana taimaka wa matan da aka ci zarafinsu.

**Hadiza:** Ka tafi kawai Dauda! Ka tafi kuma kar ka sake dawowa!

**Mai ba da labari:**

Wasu 'yan abubuwa sun fi zafin a ce mutum yana kasancewa shi kaɗai, kamar a ɗora maka laifi ne na aikata wani abu bayan mawuyacin halin da mutum yake ciki. Waɗanda Hadiza ta fi ƙauna sun yi watsi da ita a daidai lokacin da take buƙatarsu. Me ta yi shirin yi nan gaba? Ku ci gaba da sauraronmu don ku ji. A halin da ake ciki kuma, har yanzu dai hankalin Mrs. Talatu, malamar su Adam, bai kwanta ba dangane da halin da Adams yake ciki, saboda haka sai ta ƙara kiranshi zuwa ofishinta.

**Fitowa ta 2: A makarantar su Adams**

**Malama Talatu:** Adams, ina kwana? Adams, ina tunanin cewa akwai wani abin da ke damunka, kuma ina cikin damuwa. Ban san abin da yake faruwa ba, amma dai saboda yadda na san ka, na san cewa kana cikin damuwa. Adams, akwai wani abin da kake so ka gaya mini ne? Duk maganar da za mu yi za ta kasance tsakanina da kai. Ina ganin za mu iya samun taimako a kan ko ma mene ne yake damunka.

**Adams:** Kawu Jammo fa? Idan ya gane fa?

**Malama Talatu:** Adams, me yake faruwa? Kawu Jammo ne? Yana musguna maka ne? Zan iya taimaka maka.

**Adams:** Malama Talatu, ni ba zan koma gida ba. Ba zan ƙara zuwa kusa da Kawu Jammo ba.

**Mai ba da labari:**
Ɗaya bayan ɗaya Adams ya faɗa wa Mrs Talatu irin cin zarafin da Kawu Jammo yake ta yi mai, da kuma yadda ya gargaɗe shi da kar ya kuskura ya faɗa wa kowa. Bayan tattaunawa mai tsawo, Mrs Talatu ta ji komai daga bakin Adams ta yadda za ta iya ɗaukar mataki. Ta san cewa Adams zai buƙaci taimako sosai dangane da abin da ya same shi, amma a yanzu ta san cewa abin da ya fi komai gare shi shi ne a samar mai kariya. Sai ta kai shi ofishin 'yan sanda inda kuma ba su yi wata-wata ba suka je suka cafko Kawu Jammo. To me kuma zai faru gaba?
Kafin mu ji abin da zai faru, bari mu sake komawa wurin Fati. Mun bar ta nan tsaye ne a gaban motar Julie bayan Julie ta gama yi musu bayani a kan su miƙe tsaye su yaƙi cin zarafi da yi wa mata fyaɗe.

**Fitowa ta 3: A makarantar su Fati**

**Julie:** Ka tsai da motar! Ka tsai da motar na ce. … Na gode. Ka jira ni. Ina so in ji abin da yarinyar nan za ta ce.

**Fati:** Ba zan iya ci gaba da jurewa ba. Na tsani kaina. Ba ni da tsafta a…

**Julie:** Ba damuwa yarinya. Ko ma mene ne za mu iya tattaunawa a kanshi. Na tabbatar da cewa za mu sami mafita. Mene ne sunanki?

**Fati:** Fati, sunana fati.

**Julie:** Shi ke nan Fati, ki kwantar da hankalinki. Kina so mu yi magana a nan ne? Ko kina so mu koma cikin makarantar?

**Fati:** A'a! Ba za mu koma cikin makarantar ba. Yana nan ciki! Ba zan iya ci gaba jure mishi ba. Ba zan iya ƙara jurewa ba. Duk abin da kika faɗa, abin da yake faruwa da ni ke nan. Mahaifiya ta ba ta san abin da yake faruwa ba. Ita tana jin daɗi ne ganin cewa kawai ina ƙoƙari a aji, amma ba ta san cewa duk wannan sakamakon ba na Allah da Annabi ba ne. Duk sanda ya taɓa ni sai in ji kamar zan yi amai.

**Julie:** Fati, ki kwantar da hankalinki! Ki bi a hankali, ki ja numfashinki, sannan ki fara ba ni labarin daga farko. Ina son in san ta hanyar da zan iya taimakonki. Idan kina jin tsoron komawa cikin makarantar ne, to ki shiga motata. Za mu kai ki ofishinmu, sannan idan muka je, sai mu shiga inda ba kowa don ki ba ni labarin duk abin da yake faruwa. Kar ki samu damuwa. Muna da komai a wurin, har ma da

likita idan kina buƙata.

**Mai ba da labari:**
Daga nan sai hankalin Fati ya fara kwantawa. Sai ta gane cewa yanzu ta samu wadda za ta iya magana da ita ba tare da ta ji tsoro ba. Sai ta ƙagara ta shiga motar su tafi. Amma kafin ta yi haka, kwatsam, sai ga Malam Tanko a gefensu.

**Tanko:** Fati! Me kike yi a nan?

**Julie:** A'a, a yi haƙuri Malam Tanko, gaskiya laifina ne. Ni na tsai da ita a nan. Amma ina ganin cewa Fati …

**Fati:** A'a, A'a! A'a, Malam Tanko… ina so ne in tambaye ta wani abu kafin ta tafi.

**Tanko:** Kuma wannan abin ba zai iya jira ba? Ko kuma ba za ki tambaye ni ba? Ba ki ji an kaɗa ƙararrawa ba ne?

**Julie:** Malam, kamar yadda na ce …

**Tanko:** Malama Julie, don Allah kar ki sa bakinki a cikin wannan magana! Na ƙyale ki kin zo makarantata, kuma na ba ki damar yin magana, sannan kuma kina so ki ɗauki ɗaya daga cikin dalibata ki tafi da ita ba tare da izinina ba? Kin san nauyin wannan laifin kuwa?

**Julie:** Malam Tanko, ba niyyata ba ce in fitar da yarinya daga makarantar ba tare da wani ya sani ba. Fati ta kawo kanta ne wurinmu, kuma ina ganin tana da dalili.

**Tanko:** Fati! Maza ki koma aji. Yanzun nan! Kuma in an tashi, ki zo

ki same ni a ofis ɗina. Kina jina?

**Fati:** To Malam.

**Tanko:** Malama Julie, ina ba ki shawarar ki fice daga cikin makarantar nan kafin in ɗauki wani mataki. Kuma ina fata kin gane cewa wannan shi ne na ƙarshe da za a ba ki damar shigowa cikin makarantar nan.

**Julie:** Ka yi haƙuri, Malam Tanko. Don Allah kar ka huce haushinka a kan Fati. Tana buƙatar a taimake ta. Kuma ina tunanin…

**Tanko:** Ni fa na gaya miki. Sai an jima!

**Julie:** Kash!

**Mai ba da labari:**

Ga dukkan alamu dai ya ci nasarar dakatar da Fati daga faɗa wa Julie cewa shi ne mai aikata laifin. Ko kuma haka yake tunani. Sai dai Julie ta shiga motarta kuma suka kama hanyarsu. Amma ba su yi nisa ba kafin Julie ta gane gaskiya.

**Julie:** Kash! Wayyo Allahna! Mene ne nake yi haka ne? Juya motar nan mu koma da sauri! Juya motar! Mu yi sauri mu koma makarantar da wuri. Malam Tanko ne yake cin zarafin yarinyar nan da muka yi magana da ita yanzun nan! Ya kamata in gane haka ta yadda yake magana.

**Mai ba da labari:**

A yayin da Julie ta kama hanyarta ta komawa makarantar su Fati don ta ƙwato

ta a hannun Malam Tanko, shi kuwa Kawu Jammo yana can a hannun jami'an 'yan sanda, inda suka kama shi kamun wulaƙanci.

**Fitowa ta 4: A caji ofis**

**Ofisa:** Wato kai ne kake ta cin zarafin ƙananan yaranmu ko?! Dube ka, ko kunya ba ka ji!

**Jammo:** Ofisa, wannan yaron ƙarya yake min. Ku tambayi mahaifiyarshi. Za ta faɗa muku cewa wannan babban kuskure ne.

**Ofisa:** Rufe mana baki! Duk abin da ka ƙara faɗa daga yanzu, za a yi amfani da shi a matsayin shaida gare ka a kotu. Jammo, mun kama ka da laifin cin zarafi, da wulaƙanta yaro ɗan ƙarami. Za ka kasance a kulle har sai mun gama gudanar da bincikenmu a kanka. Kai Ofisa, ka rufe min ƙofar nan!

**Mai gabatarwa:**
To masu sauraronmu, yau nan shirin zai dakata. Sai ku tare mu a shiri na gaba domin jin yadda za ta kaya a ɓangaren waɗannan mutane dabam-dabam da ci zarafinsu ta hanyoyi dabam-dabam.
Kafin nan kuna iya ziyartar adireshinmu na yanar gizo, wato dw.de/lbe domin ƙarin haske ko kuma sake sauraron wannan shirin. Ana iya ziyartar adireshinmu na Facebook. Sai mun sadu a shiri na gaba. A huta lafiya.